رسالةٌ في

سجود السهو

Risalah Akan Sujud As-Sahw

Shaykh Muḥammad ibn Ṣāliḥ al-ʿUthaymīn

Mai Tarjama: Abū Firdaws 'AbdurRahman Al Mu'alimi

Markaz-us Sunnah
NIGERIA

Risalah Akan Sujud As-Sahw

Shaykh Muḥammad ibn Ṣāliḥ al-ʿUthaymīn

Mai Tarjama: Abū Firdaws 'AbdurRahman Al Mu'alimi

Markaz-us Sunnah
NIGERIA


بسم الله الرحمن الرحيم

© Markaz-us-Sunnah Nigeria

Wannan wallafar an yi ta kyauta ne a muhallin na'ura ko salula. Za a iya buga shi (printing) don amfanin mutum ɗaya ko da yawa wanda za a yaɗa kyauta, ba a yadda a yi wani sauyi ko wane iri a wannan bugun na'urar ba, ko a yi amfani da shi wajen kasuwanci ba tare da neman izini wajen masu tarjama ko mawallafa ba.

Domin neman ƙarin bayani a tuntuɓe, ta hanyar turo wasiƙa ta email: markazussunnahnigeria@gmail.com

Ta hanyar sada zumunta

@ Markaz-Us-Sunnah Nigeria

Abubuwan da ke ciki

Abubuwan da ke ciki 3

Gabatarwa 4

Sabubban Sujjadar rafkanwa 6

Na farko: Kari 6

Na biyu: Ragi 11

Na uku: Shakku 16

Shaka a cikin sallah 17

Shakku a cikin sallah wanda ya faru lokacin da ya wuce 21

A Taikache 29

Sujjada rafkanwa ga Mamu 31

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah mahaliccin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata akan annabin mu Muhammad wanda ya isar da manzanci, da mazauna gidan sa , sahabban sa da tabi'ai har zuwa ranar tashin alkiyama.

Bayan haka;

Mafi yawanci daga cikin mutane suna jahiltar hukunce-hukuncen da su ka shafi sujjada ta rafkanuwa a cikin sallah.

Daga cikin su, akwai masu barin sujjada ta rafkanuwa a lokacin da yake wajibi, ko masu sujjada ba a muhallinta ba, ko ma su sanya

sujjadar gabanin sallama alhali muhallinta ita ce bayan sallama, ko ma su yin sujjada bayan sallama alhali muhallinta bayan gabanin ta.

A dalilin haka ya kasance cewa sanin hukunce-hukuncen ta na da muhimmanci sosai, musamman ga limamai waɗanda mutane suke masu koyi da su, kuma suka ɗauki wannan nauyi a cikin koyon abin da aka shar'anta a cikin sallar su wadda su ke jagorantar Musulumai a cikin ta.

Duba da hakan, ina mai kaunar gabatarwa zuwa ga 'yan uwa na waɗansu hukunce-hukunce wanda su ka shafi wannnan babi. Ina nema daga Allah maɗaukakin Sarki ya sa ya amfanar da bayin sa muminai. Ina mai fadi bayan neman taimakon Allah maɗaukakin

Sarki, kuma nema daga gare Shi dacewa da fadin abin da yake daidai.

Sujjud-us-Sahwi

Sujjada ce guda biyu wadanda mai sallah zai aikata su domin cike gurbin wani kuskure wanda ya faru a cikin sallar sa a dalilin rafkanuwa.

Sabubbanta guda uku ne: Kari, Ragi da kuma shakku.

Na Farko: Kari

Idan mai sallah a cikin sallar sa yayi kari a cikin tsayuwa, zama, ruku'i ko sujjada da ganganci, to! sallar sa ta lalace. Amma idan ya kasance akan mantuwa kuma bai tuna ba har sai lokacin

da ya idar da sallah, to! babu komai akan sa fa ce sujjada ta rafkanuwa kuma sallar sa tana nan.

Misali Akan Hakan

Mutum yayi sallar Zuhr raka'o'i guda biyar, kuma bai tuna cewa yayi ƙari ba fa ce a lokacin da yake a cikin tahiya, zai cika tahiyar sa yayi sallama, sannan yayi sujjada ta rafkanuwa sai ya sallame.

Dalilin Hakan:

Hadisin Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara ma shi yarda, cewa lallai manzon Allah yayi sallar la'asar raka'a biyar. Sai aka ce ma sa: shin anyi ƙari a sallah ne? Sai ya ce: me kuke nufi da hakan? Suka ce: Ka sallaci raka'a biyar, sai yayi sujjada guda biyu bayan sallama.

[Bukhari da Muslim sun yi ittifaki wurin fitar da shi]

A cikin wata ruwaya, ya hada kafafuwan sa guda biyu ya fuskanci alkibla, sai yayi sujjada guda biyu sannan yayi sallama.

Sallama Gabanin Idar Da Sallah

Sallama gabanin idar da sallah na daga kari a cikin sallah {fuskar kasancewa daga kari shi ne yayi sallama kafin idar da sallah}

Idan mai sallah yayi sallama gabanin idarwar da gangan, to! sallar sa ta lalace. Idan kuma ya kasance mantuwa ce kuma bai tuna ba fa ce bayan wani lokaci mai tsawo, zai maimata wata sallar sabuwa.

Idan kuwa ya tuna bayan lokaci kadan, kamar bayan minti biyu ko uku, zai cika sallar sa yayi

sallama, sannan yayi sujjada ta rafkanuwa sai yayi sallama.

Dalilin Haka:

Hadisin Abu Hurayrah Allah ya ƙara ma shi yarda, cewa lallai manzon Allah ya jagorance su a sallah ta Zuhr ko la'asar, sai yayi sallama bayan yayi raka'a guda biyu, ya fita da gaggawa ta kofar masallaci. Sai suka cewa, an yi ragi a cikin sallah. Sai manzon Allah ya hau wata bishiya a cikin masalllaci, yana mai jingina a gare ta kamar yayi fushi, sai wani mutum ya tashi ya ce: Ya manzon Allah, shin ka yi mantuwa ko kuwa an yi ragin sallah?

Sai manzon Allah yace: ban yi mantuwa ba haka kuma ban yi ragi ba. Sai mutumin yace: tabbbas haƙiƙa kayi mantuwa. Sai manzon Allah yace da sahabbai: shin abinda yake faɗi gaskiya ne?

Suka ce: E, sai manzon Allah yayi gaba ya sallaci abin da ya rage na daga sallarsa sannan yayi sallama, sannan yayi sujjada guda biyu.

[Bukhari da Muslim sunyi ittifaki a wurin fitar da shi]

Idan kuma limami yayi sallama gabanin sallama, kuma an samu daga cikin mamu wanda ya rasa wani abu na daga sallah, kuma suka tashi domin ramuwar abin da ya kubuce musu, sannan limamin ya tuna cewa da wata tangarɗa a cikin sallar sa, sai ya tashi domin kawo ta, to! lallai su mamu waɗanda suka tashi domin ramuwar abin da ya kuɓuce ma su, su na da zaɓi tsakani ko su cigaba da ramuwar abin da ya kuɓuce ma su sannan suyi sujjadar rafkanuwa, ko kuma su dawo tare da limamin su yi koyi da shi, sannan bayan ya sallame sai su

rama abin da ya kuɓuce ma su, sai suyi sujjada ta rafkanuwa bayan sallama. Wannan shi ne mafi dacewa kuma mafi karfi.

Na Biyu: Ragewa

A. Ragewa A Cikin Rukunnai

Idan mai sallah ya rage rukuni a cikin sallar sa, kuma ta kasance kabbarar harama, ba shi da sallah, da gangan ya bar ta ko ba da gangan ba, saboda lallai sallar sa ba ta ƙullu ba. Ko da ya kasance ba kabbarar harama ba ce, lallai barin (wani rukuni) da gangan sallar na sa ta lalace.

Idan kuma mantuwa ce, to lallai dan ya kai zuwa ga dayan bangaren ta a cikin raka'ah ta biyu, zai wofintar da waccan raka’ar wadda ya bar wannan rukunin, sai ya kasance raka’ar da ya ke a kanta za ta maye gurbin waccan. Amma

idan bai isa ɗayan ɓangaren ta (raka'a ta biyu) ba, yana wajaba a kan shi ya koma zuwa ga wannan rukunin da ya bari a baya, zai kawo shi da wanda ya ke bin shi, kuma a cikin wannan hali guda biyu, yana wajaba akan shi yin sujjadar rafkanuwa bayan sallama.

Misalin Hakan:

Mutum ya yi mantuwa bai yi sujjada ta biyu ba a cikin raka'a ta farko, sai ya tuna hakan alhali ya samu kan shi yana zaune tsakanin sujjada guda biyu a cikin raka'a ta biyu, zai wofintar da raka'a ta farko, sai raka'ar shi ta biyu ta dawo matsayin ta ɗaya (wato ya kirga ta a matsayin raka'a ta farko), ya cika sallar sa gini akan ta sannan ya yi sallama. Sai ya yi sujjada ta rafkanuwa, sannan ya yi sallama.

Wani Misali na Daban

Mutum ya manta bai yi sujjada ta biyu ba kuma kuma bai zauna kafin raka'a ta biyu, sai ya tuna hakan bayan ya riga ya ɗago daga ruku'in raka'a ta biyu, to lallai zai dawo sannan ya zauna sai ya yi sujjada, sannan ya cika sallar sa sai ya yi sallama, sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

B. Ragi A Cikin Wajibi

Idan mai sallah ya bar abinda ya ke wajibi na daga cikin wajibai na sallah da gangan, sallar sa ta lalace.

Idan kuma ya kasance ya yi mantuwa ne (na wajibi), sai ya tuna kafin ya taso daga ɓangaren ta zuwa ga raka'a ta gaban ta, zai dawo ya kawo ta, sannan ya cika sallar sa sai ya yi sallama,

sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

Amma idan ya tuna ta bayan ya riga da kaiwa ga rukuni na gaba, wannan wajibin zai fadi kuma ba zai koma gare shi ba, zai cigaba da sallar sa, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa kafin ya yi sallama.

Misalin Hakan

Mutum ya ɗago daga sujjada ta biyu a cikin raka'a ta biyu, domin tashi wa zuwa ga raka'ah ta uku alhali ya yi mantuwa da tahiya ta farko, sai ya tuna kafin ya tashi, abinda zai yi shi ne ya tabbata a zauna, sai ya yi tahiyar sa, sannan ya cika sallar sa kuma babu komi akan sa. Amma idan ya tuna bayan ya riga ya tashi amma ba daidaita a tsaye ba, zai dawo, ya zauna sai yayi tahiya, sannan ya cika sallar sa sai ya yi sallama,

sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sannan ya yi sallama.

Idan ya tuna bayan ya riga ya daidaita a tsaye, yin tahiya ta fadi akan shi, ba zai koma zuwa gare ta ba, zai cika sallar sa, sannan zai yi sujjadar rafkanuwa kafin sallama.

Dalili A kan Haka

Abin da Bukhari ya ruwaito da makamancin sa daga Abdullah dan Buhainah Allah ya kara ma shi yarda; cewa lallai manzon Allah ﷺ ya jagorance su sallah ta Azahar, sai ya tashi tsaye bayan ya sallaci raka'a ta biyu ba tare da ya zauna ba; abin nufi bai yi zaman tahiyar farko ba, sai mutane suka tashi tsaye tare da shi har ya idar da sallah, sai mutane suka kasance suna jiran sallamar sa, ya yi kabbara a yayin da ya ke zaune, sai ya yi sujjada guda biyu kafin ya yi sallama, sannan ya yi sallama.

Na Uku (3): Shakku

Shi ne rashin iya rinjayar tsakanin abubuwa guda biyu wadanda suka faru.

Ita shakka ba'a la'akari da ita a cikin ibadu a wurare guda uku:

Na farko: idan ta kasance kawai ta bijiro ne a matsayin wahami ce, ba ta da hakikani, kamar waswasi.

Na biyu: idan ta yawaita tare da mutum har ta kai ga baya iya aikata wata ibada fa ce sai a cikin ta shakka ta bijiro.

Na uku: Idan ta kasance bayan idar da aiki na ibadah, ba'a la'akari da ita matukar babu yakini a cikin al-amarin, zai yi aiki da abin da ya ke da yakini a kai.

Misalin Haka

Mutum ya yi sallar Azahar, a lokacin da ya idar daga sallar sa sai ya yi shakku, shin raka'a uku ya yi ko biyar, ba zai yi la'akari da wannan shakkar ba face idan lallai yana da yaƙini cewa lallai raka'a uku ce, to a nan zai cika sallar sa idan lokaci bai ƙure sosai ba, sannan ya yi sallama, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa, sannan ya yi sallama. Idan lallai bai tuna ba, face bayan wani lokaci mai tsawo, zai maimaita wata sallar sabuwa.

Shakku a cikin waɗansu wurare na daban, wanda ba guda ukun nan ba, to lallai za su yi tasiri. Shakka a cikin (wuraren) ba sa fita daga waɗanan halaye guda biyu:

1) Hali na farko: abu ya yi rinjaye a wurin sa tsakanin abubuwa guda biyu, zai yi aiki da abinda ya ke mafi rinjaye a wurin sa, sai ya

cika sallar sa sai yayi sallama, sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

Misalin Hakan

Mutum yana sallar Azahar, sai ya yi shakka a cikin wata raka'a ya ke, shin ta biyu ce ko ta uku, amma sai yafi rinjaye a gare shi cewa ta uku ce, to lallai zai sanya ta kasance ta ukun, sai ya kawo raka'a daya bayan ta, sai yayi sallama, sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

Dalilin Hakan:

Abinda ya tabbata a cikin Sahihayn da wanin su daga Hadisin Abdullahi ɗan mas'ud Allah ya ƙara ma shi yarda cewa lallai manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbbata a gare shi ya ce: idan ɗayan ku ya yi shakku a cikin sallar sa, ya yi kokarin rinjayar daidai, sai ya cika sallar sa

a akai, sannan ya yi sallama, sannan ya yi sujjada guda biyu. [Wannan shine lafazin Bukhari]

2) Hali na Biyu

Shi ne ya kasa rinjayar da ɗaya daga cikin abubuwa guda biyu, zai yi aiki da yaƙini a anan; gini a kan mafi ƙaranci, sai ya cika sallar sa gini akan wannan, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa kafin sallama sannan ya yi sallama.

Misalin Hakan

Mutum ya na sallar la'asar, sai ya yi shakku a cikin ɗaya daga cikin raka'o'i shin ta biyu ce ko ta uku ce, kuma ya kasa rinjayarwa, shin ta biyun ce ko ta ukun, a nan zai sanya ta a matsayin ta biyu, sai ya yi tahiya ta farko, sai ya kawo a bayan ta raka'o'i guda biyu, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

Dalili A Kan Hakan:

Abinda Muslim ya ruwaito daga Abu Sa'eed al-Khudri Allah ya ƙara ma shi yarda, cewa lallai manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gare shi ya ce:

Idan ɗayan ku ya yi shakka a cikin sallar sa, kuma ya rasa raka'a nawa ya yi, uku ko huɗu? Zai jefar da kokwanto, sai ya yi gini akan yaƙini, sannan ya yi sujjada guda biyu kafiin ya yi sallama. Amma idan ya kasance ya sallaci raka'o'i guda biyar ne, za su yi masa ceto a cikin sallar sa, amma idan ya kasance ya kawo ta cikakkiya raka'a huɗun, za su kasance abin ƙarfafawa gare shi akan shaidan.

Daga Cikin Misalai Na Shakku

Idan mutum ya shigo kuma liman (Imam) yana a cikin ruku'i, to a nan lalle zai yi kabbara ta harama alhali yana mai daidaituwa a tsaye, sa'annan ya yi ruku'i.

A daidai wannan lokacin baya fita daga daya daga cikin wannan halaye;

1) Na farko: lallai ya kasance kuma ya tabbatar da ya riski liman a cikin ruku'i kafin ya ɗago daga gare shi (ruku'in). Sai ya kasance ya riski raka'a, kuma karatu na suratul Fatiha zai faɗi a kan shi.
2) Na biyu: shine lallai ya tabbata cewa liman ya ɗago daga ruku'i kafin ya iske shi a cikin shi. To a nan raka'a ta kubuce masa.
3) Na Uku: shi ne a yanayin da ya yi shakku; shin ya riski liman a cikin ruku'un sa, sai ya kasance wanda ya riski raka'a ko kuwa lallai

liman ya ɗago daga ruku'i kafin ya same shi, sai ya kasance bai riski raka'a ba.

Amma idan lallai ta yi rinjaye a gare shi ɗaya daga cikin waɗannan, zai yi aiki da abinda yafi rinjaya, sai ya cika sallar sa ya sallame. Sannan bayan hakan zai yi sujjada ta rafkanuwa ya yi sallama, amma face kawai idan bai rasa wani abu na daga sallah ba, to lallai a nan babu wata sujjada a kansa a cikin wannan halin.

Amma idan kuwa ya kasa rinjayarwa daga ɗaya daga cikin wannan al'amari, zai yi aiki da abinda ya ke da tabbaci a kai; wanda kuwa shi ne, cewa lallai raka'a ta kuɓuce ma shi, sai ya cika sallar sa akan hakan, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa gabanin ya yi sallama, sannan ya yi sallama.

FA'IDAH

Idan ya yi shakka a cikin sallar sa, sai ya gina a kan yaƙini ko kuwa zuwa ga abin da yake mafi rinjaye a gare shi, gwargwadon bayanin da mu ka yi a baya, sannan sai ya bayyana a gare shi cewa abin da ya aikata shi ne daidai a halin da yake cikin, kuma lallai cewa babu ƙari ko ragi a cikin sallar sa, sujjada ta rafkanuwa ta faɗi a kan shi, wannan shi ne abin da ya ke shahararre a mazhabi, domin daukewar abin da ya ke janyo sujjadar, ita ce shakka.

Wadansu kuma suka ce. Ba ta faɗuwa a kan shi domin nuna ƙaskanci ga shaiɗan domin faɗin manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ... kuma idan ya kasance ya cika sallar sa ta raka'a hudu, zata kasance (ita sujjadar) ƙaskanci ga shaidan. Saboda ya gabatar da wani ɓangaren sallar sa mai shakku a

cikin ta, kuma wannan zance shi ne mafi rinjaye.

MISALIN HAKAN

Mutum yana sallah, sai ya yi shakku a cikin raka'a, shin ta biyu ce ko ta uku?

Kuma babu abin da ya rinajaya dage gare shi tsakanin waɗannan guda biyun, sai ya sanya ta kasance ta biyu sai ya cika sallar sa akan ta, daga baya sai ya bayyana a gare shi cewa ta biyu ce, babu sujjada akan shi akan abin da ya shahara a cikin mazhabi, kuma akan shi ne ya yi sujjada guda biyu gabanin sallama akan zance na biyu wanda muka rinjayar.

SUJJADAR RAFKANWA AKAN MAMU (MASU SALLAH BAYAN LIMAN)

Idan liman ya yi mantuwa, yana wajaba akan masu sallah a bayan shi (liman) da su yi koyi da shi a cikin sujjada ta rafkanuwa domin fadin manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi

- Lalli an sanya maku liman domin ku yi koyi da shi, kada kuyi saɓani akan haka, har zuwa fadin sa, 'idan yayi sujjada kuma kuyi sujjada' [Bukhari da Muslim sun yi ittafaki a kan wannan hadisi daga Abu hurairah Allah ya ƙara ma shi yarda]

Sujjadar liman ta rafkanuwa idan gabanin sallama ce ko kuwa bayan sallama ce, ta na wajaba akan mamu koyi da shi, face idan ya kasance masbuqi (wanda bai riski wani sashe na sallar ba) saboda lallai shi ba zai bi shi ba a cikin sujjada ta bayan salla ba, saboda uzurin da ke gare shi. Shi masbuqi ba zai iya sallame wa ba tare da limamin sa ba. A kan haka, zai gabatar

da abin da ya rasa sai ya sallame sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa sai ya yi sallama.

MISALIN HAKAN

Mutum ya shiga sallah tare da liman a cikin raka'a ta ƙarshe, kuma ya kasance akan limamin akwai sujjada ta rafkanwa bayan sallama. Idan limami ya yi sallama, shi wannan masbuqi zai mike domin kawo abin da ya rasa na sallah, ba zai yi sujjada tare da limami ba, bayan ya kawo abin da ya rasa ta sallah, sai ya yi sujjada bayan sallama.

Amma idan shi mamu ya yi mantuwa (da kan shi) ba tare da liman ba, kuma babu abin da ya kuɓuce masa na sallah, babu sujjada akan sa saboda lallai idan ya yi sujjadar tasa, zai kasance ya saɓawa liman, da tangarda a wurin koyi da liman, saboda sahabbai Allah ya ƙara masu

yarda, ba su yi tahiya ta farko ba a ya yin da manzo Allah ya yi mantuwa, sun miƙe tare da shi kuma basu yi zama ta tashahhudi ba, domin lura da koyi da rashin saɓawa akan sa.

Amma idan ya rasa wani abu na sallah, sai ya yi mantuwa tare da limamin sa, ko kuwa a cikin abinda yake ramawa na sallah bayan yankewar sallar sa da ta liman, sujjada bata faɗuwa akan shi, zai yi sujjadar rafkanwa bayan ya kawo abin da ya rasa na sallah gabanin sallama ko kuwa bayan sallama, gwargwadon bayanan da muka yi a baya.

MISALIN HAKAN

Mamu yayi mantuwa fadin, Subhana Rabbiyal-Adheem a cikin ruku'i , kuma babu abin da ya kuɓuce ma shi na sallah, to a nan babu sujjada akan sa.

Amma idan ya rasa raka'a ko raka'o'i, to zai rama su sannnan ya yi sujjada ta rafkanuwa gabanin sallama.

MISALI NA DABAN

Mamu yana sallah ta Azahar tare da liman, yayin da liman ya miƙe zuwa ga raka'a ta hudu, mamu shi ya zauna tunani a nashi zaton cewa ita ce raka'a ta karshe. Bayan da ya bayyana a gare shi liman ya miƙe tsaye, sai shi ma ya miƙe a tsaye. Idan ya kasance babu abinda ya kuɓuce ma shi na sallah ba, to babu sujjada akan sa. Amma idan ya kasance haƙiƙa ya rasa raka'a ko raka'o'i, to zai rama su ya yi sallama, sannan ya yi sujjadar rafkanuwa sai ya yi sallama.

Wannan sujjada kuwa domin zaman da ya yi na ƙari a yayin da liman yana miƙe a tsaye a raka'a ta hudu.

A TAKAICE

Yana mai bayyana a gare mu abubuwa kamar haka daga abinda ya gabata.

Cewa sujjada ta rafkanuwa ta kan kasance a wadansu lokuta gabanin sallama ko bayan sallama.

Yana kasance wa ne gabanin (kafin) sallama a wurare guda biyu:

NA FARKO

Idan ya kasance ragi ne domin hadisin Abdullah dan Buhaynah Allah ya kara ma shi yarda, lallai manzon Allah ya yi sujjada ta rafkanuwa gabanin salllama a ya yin da yi mantuwar tahiyar farko. Lafazin hadisin ya riga ya gabata.

NA BIYU

Idan ya kasance akan shakku ne, kuma babu abinda yake mafi rinjaye akan ɗaya domin hadisin Abu Sa'eed al-Khudri Allah ya ƙara ma shi yarda; dangane da wanda ya yi shakku a cikin sallar sa, kuma bai san nawa ne ya sallata ba? Uku ko hudu?

Sai manzon Allah ya yi masa umurni da yin sujjada guda biyu gabanin sallama. Lafazin hadisin ya riga ya gabata.

Sujjada ta rafkanuwa tana kasance bayan sallama a wurare guda biyu.

NA FARKO

Idan ya kasance akan ƙari ne domin hadisin Abdullah ɗan Mas'ud Allah ya ƙara ma shi yarda, a yayin da manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya sallaci Zhuhr raka'a biyar, sai aka tunatar da shi

bayan ya riga da ya yi sallama, sai ya yi sujjada guda biyu sannan ya yi sallama, kuma baiyi bayani ba shin wannan sujjadar ta shi da ya yi bayan sallama domin rashin sanin sa na cewa anyi ƙari ne face bayan ta, haka ya ke nuni cewa hukunci a sake ya ke. Kuma nuni cewa lallai sujjada akan ƙari yana kasancewa ne bayan sallama, alhali ya san da ƙarin gabanin sallama ko na bayan sallama.

DAGA CIKI

Idan ya yi sallama gabanin cika sallar sa alhali mantuwa, sannan ya tuna sai ya cikata, toh lalle ya yi ƙari na sallama a ya yin da ya ke sallama, zai yi sujjada bayan sallama domin hadisin Abu Hurayrah Allah ya ƙara ma shi yarda, a ya yin da manzon Allah ya yi sallama a cikin sallah ta Azahar ko la'asar daga raka'a biyu, sai aka tunatar da shi, ya mike ya cika sallah sai ya yi

sallama, sannan ya yi sujjada ta rafkanuwa ya yi sallama. Lafazin hadisin ya riga ya gabata.

NA BIYU

Idan ya kasance a kan shakka, zai rinjayar da ɗaya daga ciki domin hadisin Ibn Masud Allah ya ƙara ma shi yarda, lallai manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya yi umurni ga wanda ya yi shakka a cikin sallar sa ya yi ƙoƙarin rinjayar da abinda yake daidai , sai ya cika sallar sa akan haka, sannan ya yi sallama sai ya yi sujjada.

Idan rafkanuwa guda biyu suka haɗu, ta farkon ya kamata a yi mata sujjada gabanin sallama, ta biyu kuma bayan sallama. A wannan hali, hakika malamai sun faɗi cewa, zai sanya ta gabanin sallama ta yi galaba , sai ya sallama akan hakan.

MISALI HAKAN

Mutum yana sallar Azahar, sai ya miƙe ga raka'a ta uku, alhali bai yi zaman tahiya ta farko ba, ya yi zama a cikin raka'ah ta uku tsammanin sa ta biyu ce, sannan daga baya ya tuna cewa ta uku ce, to lallai a nan zai mike sai ya kawo raka'a daya, sai ya yi sujjada ta rafkanuwa sananan ya yi sallama.

Saboda shi wannan mutumin, ya bar tahiya ta farko, ita kuwa sujjadar ta ana kawo ta ne gabanin sallama. Sai kuma ya sake ƙari na zaman wanda ya yi a cikin raka'a ta uku, ita kuwa sujjada ta bayan sallama ce. A nan sai ya sanya sujjada gabanin sallama ta yi galaba, Allah ne mafi sani.

Allah mu ke roƙo da ya datar da mu da 'yan uwan mu musulmai fahimtar littafinSa, da Sunnar manzonSa tsira da amincin Allah su

ƙara tabbata agare shi, da aiki da su a zahiri da baɗini, a cikin Aƙidah, Ibadah, Mu'amala da kyautata rayuwar mu baki ɗaya. Lallai Allah mai karamci ne.

Dukkan godiya da yabo sun tabbata ga Allah ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata akan manzon Allah, da alayen sa da sahabban sa baki daya.

رسالةٌ في

سجود السهو

Risalah Akan Sujud As-Sahw

مركز السنة بنيجيريا
Markaz-us Sunnah
NIGERIA